# Hausa - Soja Littattafai - Soldiers Scriptures

## Afisawa 6:10-18

10 A ƙarshe kuma, ku ƙarfafa ga Ubangiji, ga ƙarfin ikonsa. 11 Ku yi ɗamara da
dukan makamai na Jehovah, don ku iya dagewa gāba da kissoshin Iblis. 12 Ai,
famarmu ba da 'yan adam muke yi ba, amma da mugayen ruhohi ne na sararin
sama, masarauta, masu iko, da waɗanda ragamar mulkin zamanin nan mai
duhu take hannunsu. 13 Saboda haka, sai ku ɗauki dukan makamai na
Jehovah, domin ku iya dagewa a muguwar ranar nan, bayan kuma kun gama
kome duka, ku dage. 14 Saboda haka fa ku dage, gaskiya ta zama ɗamararku,
adalci ya zama sulkenku, 15 shirin kai bisharar salama ya zama kamar takalmi a
ƙafafunku. 16 Banda waɗannan kuma, ku ɗauki garkuwar bangaskiya, wadda
za ku iya kashe dukan kiban wutar Mugun nan da ita. 17 Ku kuma ɗauki
kwalkwalin ceto, da takobin Ruhu, wato Maganar Jehovah, 18 a koyaushe kuna
addu'a da roƙo ta wurin ikon Ruhu ba fāsawa. A kan wannan manufa ku tsaya
da kaifinku da matuƙar naci, kuna yi wa dukan tsarkaka addu'a.

## Zabura 91

1 Duk wanda ya je wurin Maɗaukaki Zai zauna lafiya, Duk wanda yake zaune a
inuwar Mai Iko Dukka, 2 Ya iya ce wa Ubangiji, “Kai ne kāriyata, da mai kiyaye
ni! Kai ne Jehovahna, a gare ka nake dogara!” 3 Hakika zai kiyaye ka Daga
dukan hatsarorin da ka ɓoye, Daga kuma dukan mugayen cuce-cuce. 4 Zai rufe
ka da fikafikansa, Za ka zauna lafiya a ƙarƙashinsu. Amincinsa zai tsare ka, ya
kiyaye ka. 5 Ba za ka ji tsoron hatsarori da dare ba, Ko fāɗawar da za a yi maka
da rana, 6 Ko annobar da take aukowa da dare, Ko mugayen da suke kisa da
tsakar rana. 7 Mutum dubu za su fāɗi daura da kai, Dubu goma kuma za su fāɗi
dama da kai, Amma kai, ba za a cuce ka ba. 8 Da idonka za ka duba, Ka ga
yadda ake hukunta wa mugaye. 9 Domin ka ɗauka Ubangiji yake kiyaye ka,
Maɗaukaki ne yake tsaronka, 10 To, ba bala'in da zai same ka, Ba za a yi wa
gidanka aikin ƙarfi da yaji ba. 11 Jehovah zai sa mala'ikunsa su lura da kai, Za
su kiyaye ka duk inda za ka tafi. 12 Za su ɗauke ka a hannuwansu, Don kada ka
buga ƙafarka a dutse. 13 Za ka tattake zakoki da macizai, Za ka tattake zakoki
masu zafin rai Da macizai masu dafi. 14 Jehovah ya ce, “Zan ceci waɗanda

suke ƙaunata, Zan kiyaye waɗanda suka san ni. 15 Sa'ad da suka kira gare ni,
zan amsa musu, Zan kasance tare da su sa'ad da suke shan wahala, Zan cece
su in girmama su. 16 Zan ba su tsawon rai lada, Hakika kuwa zan cece su.”

## Zabura 18

1 Ina ƙaunarka ƙwarai, ya Ubangiji! Kai ne mai kāre ni. 2 Ubangiji ne Mai
Cetona, Shi ne garkuwata mai ƙarfi. Jehovahna, shi ne yake kiyaye ni, Lafiya
nake sa'ad da nake tare da shi, Yana kiyaye ni kamar garkuwa, Yana kāre ni, ya
ba ni lafiya. 3 Na yi kira ga Ubangiji, Yakan cece ni daga magabtana, Yabo ya
tabbata ga Ubangiji! 4 Mutuwa ta ɗaure ni kam da igiyoyinta, Hallaka ta auko
mini a kai a kai. 5 Mutuwa ta ɗaure ni kam da igiyoyinta, Kabari kuma ya ɗana
mini tarko. 6 A shan wahalata na kira ga Ubangiji, Na yi kira ga Jehovahna
domin neman taimako. A Haikalinsa ya ji muryata, Kukana na neman taimako ya
kai kunnensa. 7 Sai duniya ta raurawa ta girgiza, Harsashin duwatsu suka jijjigu,
suka girgiza Saboda Jehovah ya husata! 8 Hayaƙi ya yi ta tuƙaƙowa daga
hancinsa, Harshen wuta da garwashi suna fitowa daga bakinsa. 9 Ya buɗe
sararin sama, ya sauko ƙasa, Tare da girgije mai duhu a ƙarƙashin ƙafafunsa. 10
Ya sauko ta bisa bayan kerubobi, Yana tafe da sauri a kan fikafikan iska. 11 Ya
rufe kansa da duhu, Gizagizai masu duhu cike da ruwa, suna kewaye da shi. 12
Ƙanƙara da garwashin wuta suka sauko Daga cikin walƙiya da take gabansa,
Suka keto ta cikin gizagizai masu duhu. 13 Sa'an nan Ubangiji ya yi tsawa daga
sararin sama, Aka ji muryar Maɗaukaki. Ƙanƙara da garwashin wuta suka
sauko. 14 Ya harba kibansa, ya watsa magabtana, Da walƙiya ya kore su. 15
Kashiyar teku ta bayyana, Tussan duniya sun bayyana, Sa'ad da ka tsauta wa
magabtana ya Ubangiji, Sa'ad da kuma ka yi musu tsawa da fushi. 16 Ubangiji
ya miƙa hannunsa daga samaniya ya ɗauke ni, Ya tsamo ni daga cikin ruwa mai
zurfi. 17 Ya cece ni daga magabtana masu ƙarfi, Daga kuma dukan masu ƙina,
Gama sun fi ƙarfina! 18 Sa'ad da nake shan wahala suka auka mini, Amma
Ubangiji ya kiyaye ni. 19 Ya fisshe ni daga cikin hatsari, Ya cece ni, don yana jin
daɗina. 20 Ubangiji yakan sāka mini, saboda ni adali ne, Yakan sa mini albarka,
don ni marar laifi ne. 21 Na yi biyayya da umarnan Ubangiji, Ban yi wa Ubangiji
Jehovahna tawaye ba. 22 Na kiyaye dukan dokokinsa, Ban yi rashin biyayya da
umarnansa ba. 23 Ya sani ba ni da laifi, Domin na kiyaye kaina daga mugunta.
24 Don haka ya sāka mini, domin ni adali ne, Gama ya sani ni marar laifi ne. 25
Kai, ya Ubangiji, mai aminci ne ga masu aminci, Kai nagari ne, cikakke ga

kamilai. 26 Kai Mai Tsarki ne ga waɗanda suke tsarkaka, Amma kana gāba da
mugaye. 27 Kakan ceci masu tawali'u, Amma kakan ƙasƙantar da masu
girmankai. 28 Ubangiji yakan ba ni haske, Jehovah yakan kawar da duhuna. 29
Yakan ba ni ƙarfin da zan fāɗa wa magabtana, Da ikon rinjayar kagararsu. 30
Wannan Jehovah dai! Ayyukansa kamiltattu ne ƙwarai, Maganarsa abar dogara
ce! Kamar garkuwa yake, ga duk mai neman taimako a wurinsa. 31 Ubangiji shi
kaɗai ne Jehovah, Jehovah ne kaɗai kāriyamu. 32 Shi ne Jehovahn da yake
ƙarfafa ni, Yana kiyaye lafiyata a kan hanya. 33 Yana sa in tabbata lafiya nake
tafiya, kamar barewa. Yana kiyaye ni lafiya a kan duwatsu. 34 Yakan horar da ni
don yaƙi, Domin in iya amfani da baka mafi ƙarfi. 35 Ya Ubangiji ka kiyaye ni, ka
cece ni, Na zama babban mutum saboda kana lura da ni, Ikonka kuma ya
kiyaye lafiyata. 36 Ka tsare ni, ba a kama ni ba, Ban kuwa taɓa fāɗuwa ba. 37
Na kori magabtana, har na kama su, Ba zan tsaya ba, sai na yi nasara da su. 38
Zan buge su har ƙasa, ba kuwa za su tashi ba, Za su fāɗī ƙarƙashin ƙafafuna.
39 Kakan ba ni ƙarfin yin yaƙi, Kakan ba ni nasara a kan magabtana. 40 Ka kori
magabtana daga gare ni, Zan hallaka waɗanda suke ƙina. 41 Suna kukan
neman taimako, amma ba wanda zai iya cetonsu, Za su yi kira ga Ubangiji,
amma ba zai amsa ba. 42 Zan murƙushe su har su zama ƙura Wadda iska take
kwashewa, Zan tattake su kamar caɓi a titi. 43 Ka cece ni daga mutane masu
tawaye, Ka naɗa ni in yi mulkin sauran al'umma, Jama'ar da ban san ta ba, ta
zama abin mulkina. 44 Za su yi biyayya sa'ad da suka ji ni, Baƙi za su rusuna
mini, 45 Za su karai, Su fita, suna rawar jiki daga kagaransu. 46 Ubangiji mai rai
ne! Yabo ya tabbata ga mai kāre ni! Jehovah ne, Mai Cetona! A yi shelar
girmansa! 47 Yakan ba ni nasara a kan magabtana, Yakan sa jama'a a
ƙarƙashina, 48 Yakan cece ni daga maƙiyana. Ka ba ni nasara a kan
magabtana, ya Ubangiji, Ka kiyaye ni daga mutane masu kama-karya, 49 Don
haka zan yabe ka a cikin al'ummai, Zan raira maka yabo. 50 Kullayaumi
Jehovah yakan ba sarkin da ya naɗa babbar nasara. Yakan nuna
madawwamiyar ƙauna ga wanda ya zaɓa, Wato Dawuda da zuriyarsa har
abada.

Pastor T. John Franklin
Church of Salvation, Healing, and Deliverance
COS-HAD.org